# ILIMI HASKEN RAYUWA

NAZARI AKAN MATSAYIN ILIMI DA AIKI DASHI A MUSULUNCI

TARE DA
(ABU MUHAMMAD)
HASSAN MUHD HASSAN

ZA'A GABATAR DA WANNAN TAKARDAR A TSARIN ILIMI DA ILIMANTARWA NA ***DAURAH*** KARO NA 6 1439/2017 KARKASHIN JAGORANCIN MAJALISSAR MALAMAI TA JAMA'ATU IZALATUL BID'AH WA IQAMATUS SUNNAH DAKE MAIGATARI LOCAL GOVERNMENT, JIGAWA STATE

*BISMILLAHIR-RAHMANIR-RAHEEM*

## GABATARWA

Musulunci addini ne da yayi kira ga neman Ilimi, kwadaitarwa akansa da bashi fifiko akan komai, mutanen farko na wannan al'ummar sun dauki ilimi da karatu da mafi kololuwar muhimmanci, suka kiyaye shi da taskace shi wannan ya sa suka kai matuka wajen ilimi da wayewa a duniya, har suka wayi gari garuruwa da biranensu su ne makoma wajen samun ilimi na addini, rayuwa da dosanar hasken shiriya[1].

Wannan takaitacciyar Qasidah zatayi nazari ne akan *Ilimi; muhimmancinsa da matsayin aiki dashi*. Allah jalla wa Alaa ya azurtamu da tsaftatacciyar fahimta ya kuma gafarta mana. Na kasa maqalah ta bayan gabatarwa zuwa bangarori guda Biyar, kamar haka;

1. 0 SHIMFIDA

Ibnu Qayyim al-Jauziyyah (Allah ya masa rahama) ya na cewa: "Mafi girman falalar abin da rai zai samu, zuciya zata riska, bawa zai samu daraja da daukaka a duniya da lahira shi ne Ilimi da Imani"[2]. Haduwar ilimi mai amfani da Imani ingantacce su ne turaku guda biyu na asalin samun aiki nagartaccce da arziki mai dorewa a wannan takaitacciyar rayuwar duniyar da dauwamammiyar rayuwar lahira.

## 2.0 MA'ANAR ILIMI DA MATAKANSA

### 2. 1 MA'ANAR ILIMI

A wannan gabar zamuyi Magana akan ma'anar Ilimi a madarar *lughah* (yaren larabci) da kuma *Isdilahi* (mahangar yaren shari'ar musulunci) a takaice.

### 2.1.1 MA'ANAR ILIMI A *LUGHAH*

Kalmar ***ILM*** a lughah ta na nufin duk abin da yake warware jahilci ya kawar dashi[3].

### 2.1.2 MA'ANAR ILIMI *ISDILAHAN*

Ilimi a mahangar shari'ah shi ne duk abin da za'a riska a hakikanin yadda yake ta fuskar karatu, bincike, nazari, gwaji ko kwarewa da taimakon wahayi ko hankali ta dayan hanyoyin riska guda biyar na dan Adam[4].

### 2. 2 MATAKAN ILIMI

Wasu ma'abota ilimi suna kallon ilimi ta nahiyar yadda ake riskar shi sai su raba shi gida biyu *Ilmud Daruriy ad-dabi'iy* da *Ilmun Nazariy al-Muktasab*. Wasu kuma suna kallon shi ta fuskar addini da rayuwa su ce akwai *Ilmus Shar'iy* da *Ilmul Kauniy*, wasu kuma ta nahiyar addini kadai suce

______________

1. Atthaqafah al-Islamiyyah na Prof. Shaukat Muhd Ulayyan sh108
2. Al-Fawa'id na Ibnu Qayyim sh137
3. Lisanul arab na Ibnu Manzur al-Ifrikiy 6/145

ILIMI HASKEN RAYUWA

akwai *Ilmul Ghayah* (Aqeedah, Qur'an, Hadith) da kuma *Ulumul Wasa'il* (Ulumul Qur'an, Usulul Fiqh, Musdalahul Hadeeth, Usulut Tareekh, Lughawiyyat d.s)[5]

Ibnu AbdulBarr (Allah ya masa rahma) ya na cewa: "Matakan ilimi a wajen dukkanin masu addini Uku ne; (a).*Ilimi mafi daukaka* shi ne na addini da babu wanda ya halatta yayi Magana a cikinsa ba tare da abinda Allah ya saukar ba a littafinsa ko harsunan manzanninsa *-Tsira da amincin Allah su tabbata agaresu-* (b).*Ilimi na tsakiya* wanda ya kunshi sanin ilimin duniya ta hanyar nazari da bincike kamar *Ilmud Dibb*[6] da *Handasah*[7] da makamantansu (c).*Ilimi na kasa* wanda yake da alaka da koyan kyautata wata kwarewa ta iya zaman duniya kamar koyan zane, tsalle-tsalle, motsa jiki, iya ruwa da sauransu[8]

Ibnu Hajar (Allah ya kara masa rahma) ya ce: "Abin da ake nufi da ***Ilimi*** shi ne na shari'ah da mukallafi zai san abin da ya wajaba akansa na alamuran ibadah, mu'amalah da sanin Allah (Tauhidi)"[9]

## 3.0 MATSAYI, MUHIMMANCI DA DARAJOJIN ILIMI

Allah Jalla wa Alaa ya kara rahama ga Shaykh Abu Abdullah Muhammad bn Sa'eed ar-Raslan, ya ambaci nassosin Qur'ani wajen 42 da hadisai ingantattu guda 41 tare da *athar* daga Magabata sama da 43 da suka zo da ambaton darajar ilimi da muhimmancinsa. Zamu takaita da ambaton Uku a kowanne bangare[10].

### 3. 1 A CIKIN AL-QUR'ANI MAI GIRMA

3.1.1 Allah Mai girma da buwaya ya na cewa: "…**Yarfa'illahullazina aamanuu minkum wallazina uutul Ilma darajaat**"[11]

Imam Shaukaniy (Allah ya masa rahama) ya ce: "Yana daga masana a cikinku da darajoji madaukaka da karamomi a duniya tare da lada a lahira"[12]

3.1.2 Allah Jalla wa alaa ya ce: "**Qul hal yastawillazina ya'alamuna wallazina laa ya'alamun, innama yatazakkaru uulul albaab**"[13]

Imam Qurdubiy (Allah ya masa rahma) ya ce Zajjaj (Allah ya masa rahma) ya ce: "Kamar yadda ba zai yiyu a daidaita mai sani da wanda bashi da sani ba, haka ba za'a daidaita mai biyayya da mai sabo ba" [14]

3.1.3 Allah jalla wa alaa y ace "**….Wa qul Rabbi zidniy Ilma"[15]**

Ibnu Qayyim (Allah ya masa rahma) ya ce: " Allah subhanahu ya umarci Annabinsa ya rokeshi Karin ilimi, wannan ya ishi ilimi daraja da sharafi, hatta Annabi *Sallallahu alaihi wa sallam* an umarce shi ya nemi karinsa"[16]

### 3. 2 A CIKIN SUNNAH INGANTACCIYA

A wannan gabar ma zamu takaitu da hadisan Fiyayyen halitta *Salawaatu Rabbiy wa salaamuhu alaihi* guda uku kadai[17]

---

4. Atthaqafah al-Islamiyyah na Prof. Shaukat Muhd Ulayyan sh104
5. Kitabul Ilm na Shaykh Uthaimin ko article din Shaykh Salman bn fahd al-Audah mai taken Pitfalls in the quest for Knowledge
6. Pharmacy da Medicine
7. Engineering (Mechanical, electrical da civil)
8. Jaami'u bayanil Ilm wa Fadluhu na Abu Umar Yusuf bn Abdullah bn Muhd bn AbdulBarr Allah ya masa rahama Juzu'I na 2 sh46
9. Fathul Baariy 1/141
10. Mai son fadadawa sai ya karanta Fadlul Ilmi wa adaabi dalabihi wa duruqi tahseelihi na Shaykh Raslan daga shafi na 40-232
11. Mujadalah: 11 12. Fathul Qadeer sh727 13. Zumar: 09
14. Al-Jami'I li Ahkaamil Qur'an 10 15. Daha:114
16. Miftahu Daarus Sa'adah 1/223
17. Domin fadadawa akan sharhi da takhrijin hadisan a duba footnote mai namba ta 10.

ILMI HASKEN RAYUWA

3.2.1 Manzon Rahmah *Sallallahu alaihi wa sallam* ya ce: ‘’**..Man yuridillahu bihi khairan yufaqqihhu fid deen, wa innama ana Qaasimun Wallahu Yu’udiy..”** [18]

Ibnu Hajar (Allah ya masa rahma) ya ce: "Babban abin fahimta a cikin wannan hadisin shi ne wanda bai samu zurfin fahimtar addini ba, an haramta masa alkhairi mai yawa”[19]

3.2.2 Manzon Shiriya *Salawaatu Rabbiy wa salaamuhu alaihi* ya ce:”**Man salaka dariqan yaltamisu fihi ilman sahhalallahu lahu dariqan ilal Jannah, wa innal Mala’ikata latada’u ajnihataha li dalibil ilmi ridan bima yasna’u, wa innal aalima layastagfiru lahu man fis samawaati wa man fil ardi hattal hiitaaanu fil maa’I wa fadlul aalimi alal aabidi ka fadlil qamari ala saa’iril kawaakibi wa innal ulamaa’a warathatul Anbiyaa’I wa innal Anbiyaa’a lam yuwarrithu dinaaran wala dirhaman Innama warrathul Ilma faman akhazahu akhaza bi hazzin waafirin”[20]**

Ibnu Qudamah (Allah ya masa rahma) ya ambata a littafinsa *Mukhtasar Minhajul Qaasideen* cewa Imaam Khaddabiy (Allah ya masa rahma) ya ce: Mala’iku da kansu suna tawadi’u domin girmama dalibin ilimi”[21]

3.2.3 Manzon Tsira *Sallalllahu alaihi wa sallam* “**Salullaha Ilman nafi’an wa ta’awwazu billahi min ilmin laa yanfa’u”**[22]

Ibnu Rajab al-Hanbaliy[23] (Allah ya masa rahma) ya ce:”Yana cikin darajar Ilimi Annabi *Sallallahu alaihi wa sallam* ya bada umarni mai karfi ga al’ummarsa akan rokon Allah ilimi mai amfani da neman tsarinsa daga ilimi marar amfani, kuma shima da kansa *Salawaatu Rabbiy wa salamuhu alaihi* ya lazimci addu’ar *Allahumma inni as’aluka ilman nafi’an wa a’uzu bika min ilmin laa yanfa’u*.[24]

3. 3 A MAGANGANUN MAGABATA

3.3.1 Umar bn AbdulAzeez (Allah ya masa rahma) ya ce:”Wanda yake wani aiki ba tare da ilimi ba, barnarsa sai tafi gyaransa yawa”[25]

3.3.2 Abu Muslimul Kaulaniy (Allah ya masa rahma) ya ce “Misalin mai ilimi a bayan kasa kamar misalin taurari ne a sama, idan sun bayyana mutane zasu shiriya idan kuwa suka boye musu zasu zama a cikin rudu” [26]

3.3,3 Imam Shafi’iy (Allah ya masa rahma) y ace: “Wanda yake nufin samun duniya, ya nemi ilimi. Wanda yake nufin samun lahira ma ya nemi ilimi”[27]

Idan muka nazarci nassosin Qur’ani Mai girma da Sunnah Ingantacciya tare da maganganun magabatan wannan al’ummar mai albarka zamu iya kallon muhimmancin ilimi a matsayinsa na jigo wanda;

- Da ilimi ne mutum zai bautawa Ubangijinsa Ibadah ingantacciya

________

18. Bukhari (71) Muslim (1037)
19. Fathul Baariy 1/285
20. Saheeh Sunan Abi Dawud 2/407
21. Mukhtasar Minhajul Qaasideen Shafi na 22
22. Silsilatus Saheehah (1511)
23. Fadlu Ilmus Salaf sh8
24. Muslim (672)
25. Jaami’ bayanil Ilm 1/27
26. al-Majmu’u 1/41
27. al-Majmu’u 1/23
28. Tsakure daga Makalarmu ta ILIMI KAMALAR DAN ADAM; Nazari akan Dabi’ar karatu a tsakanin matasa.

ILIMI HASKEN RAYUWA

- Da ilimi ne ake rayuwa cikin tsari da wayewa
- Da ilimi ne zuciya take rayuwa ta haskaka
- Da ilimi ne kaskantacce yake zama mafi daukaka cikin daukakakku
- Da ilimi ne bawa ke inganta Aqeedarsa ya tsaftace tauhidinsa
- Da ilimi ne mutum zai kama makamar kyautatuwar makomarsa
- Da ilimi ne bawa zai iya tunkude duk wani nau'I na *Shubuhaat*
- Da ilimi ne bawa zai kare kansa daga sharrin *Shahwaat*
- Da ilimi ne bawa zai haskaka gabansa yayin da duhun jahilci da bin son zuciya ya mamaye duniya
- Da ilimi ake tantance halal da haram
- Da ilimi ake kwance kai daga dabaibayin zuciya da kwakwalwa
- Da ilimi ake hutar da kwakwalwa daga daidaicewa
- Da ilimi ake habaka nazari da kaifafa hankali
- Da ilimi ake samun cikakkiyar wayewa da budadden tunani
- Da ilimi Allah ya daga darajar Kakanmu Annabi Adam *Alaihis salaam* akan Mala'iku
- Da ilimi dan Adam ke baiwa Shaidan wahala har yaci galaba akansa
- Da ilimi Allah yake bayyana addininsa
- Da ilimi kowanne al'amarin rayuwa da addini yake kammala
- Da ilimi ake samun mafita daga dukkan cikas na rayuwa
- Da ilimi ake warware dukkan kulli na cukumurdar zamantakewa.
- Da ilimi ake tantance gaskiya da waskiya
- Da ilimi ne ake tantance addinai da Aqidun kungiyoyi gurbatattu
- Da ilimi dan Adam ya banbanta da sauran halittu
- Da ilimi ladan aiyukan dan Adam suke gudana ko da baya raye
- Da ilimi ne bawa yake riskar mafi girman matsayi a duniya da mafi darajar mataki a lahira.[28]

## 4. 0 ALAKAR ILIMI DA AIKI

### 4. 1 ILIMI MAI AMFANI

Ibnu Rajab al-Hanbaliy (Allah ya masa rahma) ya ce: "Ilimi mai amfani shi ne wanda aka daureshi da nassosin al-Qur'ani da Sunnah da fahimtar ma'anoninsu, tare da takaita kai akan abin da aka rawaito daga sahabbai, tabi'ai da wadanda suka biyo bayansu"[29]

Daliban ilimi da malamai zasu iya tarayya a fagen karatu da nazari amma su banbanta a fagen riskar ilimi da samun albarkarsa ta fuskar tazarar da ke tsakaninsu na fahimtar ilimin da aiki dashi. Ilimi mai amfani shi ne wanda ya samar da tasirin aiki a zuciya ko gangan jiki.

Aiki da ilimi ya na lazimta *muraqabah* da kiyaye dokokinsa, sannan ya zama babban sababin kara kusanci ga Allah

___________

29. Fadlu Ilmus Salaf alal Khalaf sh45 30. Muhammad: 17
31. Fadir: 27 33. al-Jami'I na Khadeeb sh15
33 da 34. Sharhu Hilyatu Dalibil Ilm sh39
35. Ishara ga hadisin Abu Huraira a Sahih Muslim (5032)
32 da 36. Hilyatu Dalibil Ilm sh 37 37. Fadir: 28
38. Tafsirul Qur'anil Azeem 3/913
39. Al-Jami'u li ahkamil Qur'an 14/331
40. Fadlul Ilm na Shaykh Raslan sh625
41. Qaaf:37

ILMI HASKEN RAYUWA

da karuwar shiriya[30] Kamar yadda rashin aiki dashi ya na nesanta mutum daga amfanuwa dashi da samun albarkarsa[31]

Allah jalla wa alaa ya kara rahma ga Dr. Bakr Abu zayd ya hakaito[32] cewa: **Wa asnadal Khadeebul Baghddiy (Rahimahullahu ta'ala) bi sanadin fihi ladeefah Isnadiyyah bi riwayati Aabaa'in Tis'ah Fa qala Akhbarana Abul Faraj AbdulWahhab bn AbdulAzeez bn Harith bn Asad bn Laith bn Sulaiman bn Aswad bn Sufyan bn Zayd bn Akeenah bn Abdullahi at-tamimiy_Min hifzihi_Qala Sami'itu Abiy yaquulu: Qala Sami'itu Abiy yaquulu: Qala Sami'itu Abiy yaquulu: Qala Sami'itu Abiy yaquulu: Qala Sami'itu Abiy yaquulu: Qala Sami'itu Abiy yaquulu: Qala Sami'itu Abiy yaquulu: Qala Sami'itu Abiy yaquulu: Sami'itu Aliyyu bn Abi Dalib yaquulu: "Hatafal Ilmu bil amali fa'in ajabahu, wa illaa irtahala"** [33]

Shaykh Muhd bn Salih Uthaimin (Allah ya masa rahma) ya ce[34]: "Kenan ba makawa ayi aiki da abin da aka sani, domin idan mutum bai yi aiki da abin da ya sani ba, zai kasance a cikin wadanda za'a fara Konawa a wuta aranar Qiyama"[35]

4. 2 ILIMI NA TSORON ALLAH

Malami ba ya zama malami sai ya zama mai aiki da iliminsa, ba zai zama mai aiki da iliminsa ba sai ya lazimci tsoron Allah a bayyane da boye, wannan ne ya sa Imam Ahmad (Allah ya masa rahma) y ace: "**Aslul Ilmi Khashyatullah ta'ala"**[36]

*Khashyatullah* shi ne tsoro da aka gina shi akan ilimi da girmamawa. Allah jalla wa alaa ya na cewa: "**Innama yakhshallaha min ibadihil Ulamaa'"**[37]

Ibnu Katheer (Allah ya masa rahma) ya ce: "Ma'ana wadanda suke hakikanin tsoronsa sune ma'abota Ilimi..Domin duk lokacin da sanin Allah yake cika, ilimi akan hukunce-hukuncensa suke kammala, tohh tsoronsa zai ke girmama da yawaita"[38]

Abdullahi bn mas'ud (Allah ya kara masa yarda) ya ce: "Tsoron Allah ya wadadta ya zama ilimi, rudu da shagala sun wadata su zama jahilci" Mujahid ibn Jabar (Allah ya masa rahma) ya ce: "Masani ne kadai yake tsoron Allah" Rabee' bn Anas (Allah ya masa rahma) ya ce: "Duk wanda baya tsoron Allah, ba malami bane"[39]

5. 0 RUFEWA (KHITAMUHU MISK)

Ibnu Qayyim al-Jauziyyah (Allah ya masa rahma) ya sanya aiki da ilimi mataki mafi daukaka cikin matakan samun ilimi mai amfani guda shida, wanda rashinsa kuma yake wajabta haramtawa mutum samun ilimi mai albarka. A karkashin ayar da Allah jalla wa alaa y ace: "**Inna fi zalika la zikraa, liman kana lahu Qalbun au alqas sam'a wa huwa shaheed"**[41]

Duk falalar ilimi tazo ne akan ilimin da akayi aiki dashi, kuma da aiki da ilimi Dan adam yak e samun kamalar sa'adar rayuwar duniya da lahira.

*Allah Jalla wa alaa muke roko da sunayensa kyawawa da siffofinsa Madaukaka ya azurtamu da ilimi mai amfani, ilimi na tsoron Allah. Allah subhanahu wa ta'ala ya tsaremu da ilimin da zai zama hujja akanmu ba garemu ba.*

*Hmhmgr07@gmail.com*
*+2348144777338*
*Wed 1st Nov, 2017*

ILIMI HASKEN RAYUWA